# Kada ku ce : Allah Ya so wane ma ya so, saidai ku ce: Allah ne Ya so, sannan wane ma ya so

Daga Huzaifa - Allah Ya yarda da shi - cewa Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: "Kada ku ce : Allah Ya so wane ma ya so, saidai ku ce: Allah ne Ya so, sannan wane ma ya so".

[Ingantacce ne a baki dayan hanyoyin sa] [Abu Dawud da Nasa'i cikin alkubra haka Ahmad suka ruwaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya hana musulmi ya ce a zancensa: Allah Ya so wane ma ya so", ko Allah Ya so da wane; hakan domin ganin damar Allah da nufinSa a wawaice suke, wani ba ya tarayya daShi a cikinsu, a cikin amfani da Waw (da) a adafi alamtarwa ne na hada wani tare da Allah da daidaitawa a tsakaninsu. Saidai ya ce: Allah ne Ya so, sannan wane ma ya so, Sai ya sanya ganin damar bawa mai bi ce ga ganin damar Allah ta hanyar fadin: "Sannan" canjin "da"; domin "sannan" tana fa'idantar da bibiya da kuma jinkiri.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee